# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na farko: Ba ni da wani laifi

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Sherifat: | 'yar shekara 40 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Hadiza: | 'yar shekara 30 |
| Jummai: | 'yar shekara 25 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| Precious: | 'yar shekara 30 |
| Jammo: | ɗan shekara 45 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wani sabon jerin shirye-shiryenmu da muke kawo muku na “Ji Ka Karu” wanda aka sa wa suna “Cin Amana” wanda ke zuwa mu ku ta wannan kafar rediyo ta Deutsche Welle da ke nan birnin Bonn. Wannan shirin ya ƙunshi wani al'amari ne da ya addabi dukkan ƙasashe na duniya. Wannan al'amari dai shi ne cin zarafin 'ya'ya mata. Kamar yadda za mu ji a cikin jerin shirye-shiryen da za mu gabatar shi dai wannan al'amari na cin zarafin 'ya mace, ko tilasta ma 'ya mace yin jima'i ba ya tsaya ne a garuruwan da ake fama da yaƙi kawai ba, abu ne da ya zama ruwan dare kuma ya ke faruwa a ko'ina a duniyar nan.

Za mu sadu da wasu yara matasa da ke zaune a wani gari mai suna Mai Aduwa. Fati yarinya ce 'yar shekaru goma sha shida da ke wata makarantar kwana ta maza da mata. Sai Adam, wani yaro ɗan shekaru goma da haihuwa, wanda kuma agola ne a gidan Kawu Jammo. Sai kuma na ƙarshensu Hadiza, wata mace da ke zaune a kusa da wani jeji da 'yan ta'adda ke samun mafaka. Dukkansu za su samu kansu cikin halin cin zarafi da aka yi musu ta hanyoyi dabam-dabam, kuma za su yi ƙoƙarin gudanar da rayuwarsu ta cikin ƙunci saboda mawuyacin halin da tsinci kansu. Idan shirin ya yi nisa kuma za mu sadu da Jummai, mai aiki da wata ƙungiya mai yaƙi da cin zarafin 'ya mace.

Wannan shi ne shiri na farko a shirye-shirye goma da za mu gabatar. Za mu faro ne da lokacin da mahaifiyar Fati, Sharifat, ta kai ta makarantar da ta samu ta kwana ta maza da mata. Yanzu ga su can a ofishin Malam Tanko wanda shi ne ke kula da shashen ɗakunan kwana na ɗalibai a wannan makarantar.

**Fitowa ta 1: A ofishin Malam Tanko a makaranta**

**Tanko:** Sannunku da zuwa! Ke ce Fatima Sherifat ko?

**Fati:** E, ni ce Malam.

**Tanko:** To ko za ki buɗe akwatinki? Zan duba irin abubuwan da

kika zo da su ne.

**Sherifat:** Mene?! Malam...

**Tanko:** Sunana Malam Tanko.

**Sherifat:** Malam Tanko, wannan ai bai kamata ba. Shekarun 'yata goma sha shida. Bai kamata a ce tana da nata sirrin ba? Ina nufin cewa nan ba da daɗewa ba za ta zama cikakkiyar 'ya mace!

**Tanko:** Malama, ai wannan ba wani abu ba ne na dabam. Zan duba ne kawai saboda in tabbatar da cewa ba ta zo da wani abin da ba a yarda da shi ba. Wannan yana ɗaya daga cikin ƙa'idojin makarantar nan. Ko wane ɗa namiji da 'ya mace da suka zo karatu a wannan makarantar kwana ta Mai Aduwa sai an yi musu irin wannan dubawar. Saboda haka ko dai ki yarda da wannan ƙa'ida ko kuma ki ɗauki 'yarki ki kai ta wata makarantar. Wannan ba wani abin jayayya ba ne.

**Sherifat:** Fati, buɗe mai jakar ya gani. Amma dole ne sai ta nuna komai da komai da yake cikin jakar?

**Tanko:** To, ya kamata dai a ce na duba komai da komai a ciki. Amma kin san wani abu: a wannan karan ba zan yi haka ba. Ki rufe jakarki. Wani abu ya nuna min cewa ke yarinyar arziki ce da zan iya yarda da ita.

**Fati:** Na gode Malam Tanko.

**Sherifat:** Kamar ka sani, ai Fati yarinyar kirki ce! Kuma ba ƙoƙari kawai take da shi ba, ta iya gudu sosai. Don Allah ka

tabbatar da cewa ta shiga ƙungiyar 'yan wasan motsa jiki.

**Fati:** Kai Mama, ba fa na ƙware ba ne kamar yadda kike faɗa. Ina son gudu amma ba wai na gasa ba.

**Tanko:** To, na ji daɗin haka don makarantarmu ita ce kan gaba idan ana maganar wasannin motsa jiki ne. Kuma ko da yaushe muna jin daɗin samun ɗalibai masu jini a jika a cikin wannan ƙungiya tamu. Shi ke nan, mu je in nuna miki ɗakin kwananki, Fati.

**Sherifat:** Am, yauwa Mallam Tanko, kafin ku tafi, don Allah ina da wata tambaya ce da take damuna a zuci. Ganin cewa wannan makaranta ta maza da mata ce, akwai wata kariya kuwa ga 'yata? Na ga ga maza nan suna da yawa a ko'ina. Kuma ga shi makaranta ce ta kwana ta maza da mata a haɗe, ka ga ai dole in shiga wata damuwa ko?

**Tanko:** Malama, kina ɗaya daga cikin iyaye da yawa da suke yi mini irin wannan tambayar. Amma kada ki damu kanki. Haka ne cewa wannan makarantar kwana ce ta maza da mata, amma an raba su da waya a tsakiya. Sannan kuma akwai mai gadin da ke sa ido da daddare don ya tabbatar da cewa babu wani wanda ya saci jiki ya shiga inda matan suke. Ina tabbatar miki da cewa babu abin da zai sami 'yarki a nan.

**Sherifat:** Kai, har na ɗan ji dama-dama.

**Tanko:** Fati, biyo ni mu je. Bari in kai ki ɗakin kwananki.

**Fati:** Shi ke nan, Mama. Zan rubuto miki wasiƙa kwanan nan.

**Sherifat:** Shi ke nan 'yar Fatita. Ni ma in Allah ya yarda nan ba da daɗewa ba zan zo in duba ki. Ki ci gaba da kasancewarki yarinya ta gari fa, kin ji ko Fatita!?

**Fati:** Na ji, Mama.

**Mai ba da labari:**
Sherifat ta bar 'yarta a hannun kulawar Malam Tanko, shugaban ɗakunan kwana na wannan makarantar. Amma kana ganin cewa akwai azanci a cikin gwamutsa yara maza da mata a wuri ɗaya a makarantar kwana? Kuma ana iya yarda da malaman kuwa?
Yanzu bari mu aiyje wannan, mu kuma bari Fati ta natsa, mu leƙa wajen su Hadiza da Jummai. Waɗannan matan auren sun kasance ƙawayen juna ne tun suna ƙanana. Suna zaune ne a wani ɓangare na garin Mai Aduwa wanda ke fama da yawan samun hare-hare na 'yan ta'adda. Jummai na da ɗa jariri, sannan Hadiza tana da cikin wata biyar. A yanzu haka matan biyu sun yi tafiya mai tsawo zuwa wata rijiya su ɗebo ruwa.

**Fitowa ta 2: A rijiya**

**Hadiza**: To yaya labarin Umar, Jummai? Ya samu sauƙi yanzu ko?

**Jummai:** Hadiza, ai Umar yana can yana tsalle-tsalle sai ka ce ɗan jaririn doki. Na baro shi ne yana wasa da babanshi. Ke kuma fa? Ina ce dai ba wata matsala da cikin ko?

**Hadiza:** A'a, wallahi ba komai, lafiya ƙalau, sai dai 'yar gajiya kawai. Ai Jummai duk na ƙosa in haihu. Dauda ya ƙagara ya ga an ce shi ma ya zama baba. Shi ya fi so mu sami 'ya mace, amma ni ina ganin ɗa namiji ne.

**Jummai:** Kika ce mai gidanki ya fi son 'ya mace a maimakon ɗa namiji?

**Hadiza:** Kwarai. Akwai wata matsala ne a kan hakan?

**Jummai:** Wata matsala? Kwarai kuwa akwai matsala da hakan! Mazaje 'yan Afirka a kulli yaumin sun fi so a haifa musu 'ya'ya maza. Ni wannan Daudan naki! Ina ganin ɗan zamani ne.

**Hadiza:** A'a. Ina ganin dai ya gane cewa ne ba wani bambanci ko mace ko namiji. Abu mafi muhimmanci kawai shi ne zai dai kasance cewa ɗanmu ne. Don Allah ko za ki zuba ruwan? Bokitin ya cika.

**Jummai:** Hadiza, yau ina ganin ba zan iya jiranki ba. Zan kai wa goggota da ba ta da lafiya ruwa. Tana zaune ne a can ƙasa, saboda haka ba za mu koma tare ba. Ki yi haƙuri, na manta ne in faɗa miki tun farko.

**Hadiza:** A'a! Don Allah Jummai kar ki tafi ki ƙyale ni a nan ni kaɗai. Wurin nan yana da hatsari sosai!

**Jummai:** Haba, don Allah ki kwantar da hankalinki! Ba abin da zai same ki. Zan biyo ta gidanku gobe da safe in Allah ya kai mu, kin ga sai mu tafi ɗiban ruwa tare da ke kamar yadda muka saba. Sai an jima Hadiza. Ki gai da min da maigidanki.

**Hadiza:** To shi ke nan Jummai, kya gai da min da goggon taki. … Ya kamata in hanzarta. Ba na son kasancewa a nan ni kaɗai. A dajin can 'yan ta'addan nan fa suke ɓoyewa.

**Mai ba da labari:**
Ya fito fili dai cewa Hadiza a tsorace take, amma na me? Ya kamata a ce tana cikin tsoro haka? Ku kasance da mu domin jin amsa. Amma yanzu bari mu leƙa wani ɓangaren kasar inda dan yaron nan mai shekaru goma wato Adams, yake zaune a wani ɗan shago yana shan lemun kwalba. Yana tare da mahaifiyarsa Precious wadda a yanzu haka bazawara ce. Precious ta zo da wani namiji wanda Adams bai taɓa gani ba. Wane baƙo ne kuma wannan?

**Fitowa ta 3: A gidan cin abinci**

**Precious:** Adams, akwai wani baƙo da na ke so ku sadu. Kai Adams, mene ne haka! Ka daina wannan abin don Allah! Haba! Sakaran yaro kawai. Ina maka magana, ba ka ji. Na ce ka zo ka gai da kawunka, Kawu Jammo.

**Adams:** Hmm?

**Precious:** Na ce ka gai da kawunka!

**Adams:** Sannu Kawu. To ina ɗaya kawun?

**Precious:** Wane …? Erm… Ban sani ba …

**Jammo:** Ɗaya kawun ya yi tafiya.

**Adams:** Ni na fi sonshi fiye da sauran.

**Precious:** Kai… Eee… Na san cewa wannan ma za ka so Kawu Jammo shi ma.

**Jammo:** Karɓi nan Adams, je ka ƙara sayan wani lemo.

**Precious:** To, me ka ce?

**Adams:** Na gode.

**Precious:** Jammo, don Allah ka yi haƙuri. Kar ka damu da abin da yaron nan yake faɗi. Ina fatan dai ba ka yi fushi ba ko.

**Jammo:** A'a'a, wane irin fushi? Ina ganin yaro ne mai gaskiya, kuma haka yana da kyau. Amma ba kya ganin ya kamata a faɗa mai gaskiya? Kin san dai ni ba kawunshi ba ne. Ni zan zama kamar babanshi ne.

**Precious:** A'a'a'a, ina ganin dai ya kamata mu ƙara jira tukuna. Nan gaba ma faɗa mai idan ya ƙara saninka sosai. Na ji daɗi dai da irin fahimtar da ka nuna kuma ina fata da kai da shi za ku fahimci juna sosai.

**Jammo:** Haba, kar ki damu da wannan, Precious. Ba ni da matsala da yara.

**Mai ba da labari:**

Kalaman da Jammo ya furta irinsu Precious take son ji. Amma ta yi daidai kuwa da ta nuna yarda da Jammo da wuri haka? Nan ba da daɗewa ba za mu gane hakan. Amma yanzu, bari mu leƙa wurin Hadiza wadda a halin yanzu ta gama cika tulunta na ruwa a bakin rijiya.

**Fitowa ta 4: A rijiya**

**Hadiza:** Yauwa, yanzu tun da na cika tuluna bari in yi maza in bar wurin nan kafin…Wayyo Allahna! Ina fatan dai ba su ba ne,

ina fatan dai bayan 'yan ta'addan ba ne! Wayyo Allahna, za su gan ni, za su gan ni. In kuma suka harbe ni fa? Bari in ɓoye da sauri a nan, bari in ɓoye, bari in shigo kogon nan. Yauwa! Wayyo Allah, kada su zo neman ruwa a nan. Allah ka sa su wuce kawai! Wayyo ni kaina, wayyo Allahna! …

**Mai gabatarwa:**

A nan kuma za mu ja labulen shiri inda Hadiza ta ɓoye a cikin wani kogo a wannan shiri namu na farko a kan cin zarafin 'ya mace. Shin Hadiza za ta iya ɓoye wa 'yan ta'addan kuwa? Me zai sami Fati a sabuwar makarantarta ta kwana? Sannan za a samu daidaito kuwa tsakanin Jammo da ɗan karamin yaron nan Adams?

Don jin duk waɗannan labarai da ma wasu labaran sai a kasance da mu a shiri na gaba. Idan kuma ana so a ƙara sauraron shirin sai a neme mu ta adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ku huta lafiya.